Lallai Rana ba'a tava tsayar da ita ga wani Mutum ba sai ga Yusha'u a Dararen da ya tafi Baitil maqdis

An rawaito daga Abu Huraira, ya ce: Manzon Allah SAW ya ce: "Lallai Rana ba'a tava tsayar da ita ga wani Mutum ba sai ga Yusha'u a Dararen da ya tafi Baitil maqdis"
[Ingantacce ne] [Ahmad ne ya rawaito shi]

Babu wani Mutum da aka tava tsayar Masa da rana ba ta tsaya a falakinta sai Yusha'u Bin Nun kuma shi saurayi ne tare da Annabi Musa da yai tafiya tare da shi zuwa Khidhr lokacin da suka tafi Baitul Maqdis kuma cewa shi yaji tsoron faxuwar ta kafin ya shiga, kuma Ranar ta Kasance Jumu'a da ace ta faxi da ya shiga ne ranae Asabar kuma Yaqi a ranar haramun ne, sai ya ce da Rana ke Baiwar Allah ce nima haka, Ya Ubangiji ka tsayar da ita sai ta tsaya saboda shi har ya shiga Baitul maqdis

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/10998